Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Character of Our Times." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-1570-halin-zamani/.

# Halin Zamani

[Page 1]

Bismi l-Lāh al-Raḥmāni al-Raḥīm. Ṣalawātu l-Lāhi ʿalā Sayyidinā Muḥammad wa ʿalā ālihi wa ṣaḥbihi wa sallama taslīman. Ibtidāʾu yawm al-khamīs qabla dukhlū l-waqti l-ẓuhr

Yā Rabbanā ya Rabbanā ya Wāhidī  Allah Tabāraka Sarki Shi Ɗaya
Allah a'ɗini baṣīra Rabbanā  Natsara waƙa tahalin zamani
Kai ne Ilāhi a wannan zamani  Yaro da babba ba su ƙaunar gaskiya
Ya ƴan uwa na ga ku zo ku ji gargaɗi  In ta yi daɗi za ki ji ta ware-ware
Yau wadda ta jawo halin ƴar uwa  Kan buki, kurɗi, ba kin yi maƙaraji
In ka yi zance sai a ce ƙarya ka yi  Shirme  kuɗi shine yake zance aji
To arziƙi ku san nufin Allah ne  Allah Ka samu takun mutanen arziƙi
Mai arziƙi shine yake hango masar  Kai ba ka kuɗi ba ka hangen kasuwa

## Sana'a

Ya ƴar uwa ki riƙi sana'a kin jiya  Neman abinci yana da daɗi ƴar uwa
Rigarka wundi har da wando ɗan fara  Taguwa da hula har da takalmin Kano
In ka wadatu ka sai atamfa sabuwa  Ga tocila ko ƙin kana yawo dawa
Kai ne da zance na ga badwal harko  Ki har agogo da gorami ko ya fito
In ba sana'a ba ka samun ƴar haka  Ai sai ka ja carbi kai ta wargin zama
Yau ga abinci da mai da nama an rufo  Ai mai sana'a shi ka ci su ka sha ruwa

[Page 2]

| | |
|---|---|
| Saka da danka har da mai cin kasuwa | Neman abinci ake ta yi kuwa ƴan uwa |
| Neman tubarraki kadai ne sutura | Ga mai safili kun ji kuke bin hawa |

**Baƙuwa firāq baynī wa bayna**

**akhūnī ḥabibī**

| | |
|---|---|
| Na yi kukan rabuwa da ɗan uwa | Ga ɗan uwa mai haƙuri mai godiya |
| Ba ya fushi ba ya faɗa ga haƙuri | Komi ka ce masa sai ya fito ba gardama |
| Wallahi shi ne ya tsaya mani gaskiya | Ya ce ka ɗau himma ka bar san wasanni |
| Shi ba shi noma ba shi saukar jibi | Sai dai karatu ya riƙe shi da gaskiya |
| Shi ne ya sa wajen karatu can dawa | Wallahi sai malam ya ba ni garma ɗaya |
| Malam na huntu maza matane hanƙarami | Shi ta sa ta ƙare yana can barzahu |
| Allahu iftaḥ baba Jannata Rabbana | Ƙamshi da haske su tareshi gaba ɗaya |
| Dama Ka sa shi ciki mutanen annabi | Shi ma ya sam ceto a ranar illā lākhira |
| Wa abīhi har ikhwānihi jamʿu tas | Allāhu agfir zunubahum baki ɗaya |

**Nas ʾalu Allāh**

| | |
|---|---|
| Allāhu arzuqnī bi ḥayāti l-Musṭafā | Wa bi Shaykhi Aḥmadi mai Ɗariqā Rāshidi |
| Allāhu arzuqnī bi mālin kaza ʿilmin | Bi l-ḥubbi bayna l-nāsi Muslimi da kāfiri |
| Almalu yanfaʿ kana jin kalmar maluma | Ya malami ya mai kiyaye gaskiya |
| Kai ka wadatu ka baiwa kowa wajibi | Kar ka yi ka ce baƙo kamar baƙin kare |
| Haka malami kai ma kabar ƙin gaskiya | Wallahi ka taɓe a ranar lākhira |